# WASU HADISAI ARBA'IN GAME DA AL-QUR'ANI


Wallafar

Ahmad Bn Abdurrazaq Bn Muhammad Aal Ibrahim Al-anazy

Gabatarwar

Babban Malamin Hadisi

Salih Bn Sa'ad Al'luhaidan

Da kuma Babban Malamin Hadisi

Abdullahi Bn Abdurrahman Al-Sa'ad

Kuma Babban Malamin Hadisi Dr.

Mahir Bn Yasin Al-fahl

Kuma Babban Malami Dr.

Hamad Al-tamimi


Bugu na sha biyar

# Gabatarwar Muftin Alkali na Musamman Shehin Malamin Hadisin nan: Salih Bn Sa'ad Al-luhaidan - Allah Madaukaki ya kare shi -

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin kai

Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya saukar da littafin sa Mai Hikima da kuma Shiriya Hukunci Gaskiya da kuma Tafarki Madaidaici.An Saukar da shi ga Mafificin Halittarsa da Manzanninsa - Amincin Allah a gare su - Annabi Muhammad tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi don ya tsaya wajen isar da shi ga baki dayan su har zuwa ranar da za'a tashe su.Bayan Wannan Hakika Dana Shiekh Ahmad Bn Abdurrazak Bn Muhammad Bn Zayid Al-angari ya gabatar mun kwafi na littafinsa HADISAI ARBA'IN GAME DA AL-QUR'ANI wanda ya kunshi Falalolin Alqur'ani Maigirma da kuma abin da ya a san shi da kuma aiki da shi ta hanyar Iklasi da gasgata aiki da kuma kubutacciyar Niyya ga barin abin da zai bata ta.Kuma babu wani laifi to duk wanda yayi duba na nutsuwa ga abinda Shiekh Ahmad ya kawo a littafinsa zai same shi cewa ana matukar bukatar kwatankwacin irin wannan a wannan lokaci wanda ya yake bukatarsa, Ya wajaba ga Musulmi ya sani kuma ya kiyaye hakikanin Hukunce hukuncen Addininsa da Duniyarsa ta hanyar Alqur'ani da Ingantacciyar Sunnakuma hakika ya zo daga Dan Umar cewa shi ya ce: bama wuce Ayoyi goma har sai mun koyi Ilimi da kuma aiki da shi daga cikin suKuma Alqurani Maigirma da Sunnanar Annabi dole ne a koye su daga Bakin Malamai wadan da suka hada tsakanin Ilimi da Hadda da kuma Fahimta da kyakkyawar fahimta ta hakikanin abin da nassi yake nufi cikin manufofin Rayuwar Duniya da lahira na abinda ya hada tsakanin Maganganu da kuma Ayyuka

kuma Rubuta wadan nan hadisan Alqurani bana zaton Shiekh Ahmad yana nufin ya gama tare baki dayansu domin wasu daban da yawa sun zo suna nan a tattare a cikin Manyan litattafan Hadisi guda Shida da wajensu Kamar Musnad na Imam Ahmad da Al-musannaf Na Abdurrazak da Musannaf na Ibn Abi Shaibah, da Sahihin ibn Hibban da Musnad na Sa'id Bn Masour da wasun su na tushen Musulunci, sai dai yana nufin fadakarwa zuwa Muhimmanci da kuma falalarsa da haddace shi da kuma kyakkyawan Nazarinsa ta hanyar wa'azantuwa da Ayoyinsa ba wai don tarawa ba da kuma haddace shi da aikata shi da Hukunci da abinda yake faruwa na Hukunce Hukuncen Sababbin abubuwa sababbi da suke faruwa.

kuma ya isa Daukaka ga Mahaddacin Qur'ani cewa shi ana bashi lada kan Haddarsa , kuma qurani zai cece shi, kuma ana samun waraka da shi kuma ana samun Albarkar samunsa da shi daidai da yadda ya kyautata niyyarsa da kuma jin Tsoransa da tsantseninsa.

To Allah Madaukaki yayi Albarka a kokarin Shiekh Ahmad Al-Ibrahim Al-Angary kuma ya amfanar da Ilimin sa kuma ya kuma Karfafe shi domin cewa shi Mai yawan kyauta ne kuma Mai baiwa

Wanda ya rubuta shi

Salih Bn Sa'ad Al'luhaidan

1428/1/17 Bayan Hijira

# Gabatarwar Shehin Malami Masanin Hadisi Abdullahi Bn Abdurrahaman Al-sa'ad - Allah ya tsare shi -

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin kai

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai kuma tsira da Aminci su tabbata ga Manzon Allah tsira da Aminci su tabbata a gare shi. Bayan haka kuma

To hakika na karanta littafin Dan mu Shiekh Ahmad Bn Abdurrazak Bn Muhammad Al-Ibrahim Al-angary Allah ya datar da shi.

wacce ta tare Hadisai Arba'in na Falaloli da Hukunce Hukunce da kuma Ladaban Alqur'ani Maigirma, kuma hakika ya kyautata wajen taro su kuma ya amfanar, to Allah ya saka masa da Alkairi.

kuma wannan Maudu'i yana daga cikin Maudu'ai Muhimmai sabo da dangantakar sa da littafin Allah Maigirma da Daukaka

Kuma daga cikin Mafi girman Ayyukan neman lada wadan da Bawa zai kusanci Ubangijinsa da su Nazarin Ayayoyinsa kamar yadda Allah yace cikin littafinsa: "Littafi ne da muka saukar da shi a gareka mai Albarka don kuyi nazarin Ayoyinsa"

Ibn Al-qayyim ya ce: a cikin Fa'idodi: littafi na 1 a shafi na 3Wata Babbar Ka'idaIdan kanason Amfani da Qur'ani to ka taro zuciyarka wajen Karatunsa da jinsa, kuma kabada jinka, ka halarto da zuciyarka da wanda kake magana da shi mai tsarki, to cewa zancensa, wanda yazo ta hanyar Manzonsa.Allah Madaukaki ya ce"Lalle ne, a cikin wancan, akwai tunãtarwa ga wanda zũciyarsa ta kasance gare shi, kõ kuwa ya jẽfa saurãro, alhãli kuwa yanã halarce (da hankalinsa).Suratu Kaaf: 37

kuma wannan cewa cikar Tasirin ya kasance yana nan ne kan Tasirin abun da ake karantawa, kuma nan Mahallin karba, kuma Sharadin samun Tasirin, kuma da kore duk wani abun da zai hana hakan, kuma Ayar ta kunshi bayanin hakan baki dayan sa da dunkulallun lafazansa da gininsa, da kuma nuninsa kan Manufarsa.

Da fadinsa: Lalle ne, a cikin wancan, akwai tunãtarwaSurat Kaaf: 37Nuni zuwa ga abinda ya gabata daga farkon Sura zuwa nan kuma wannan shi ne abu mai TasiriFadinsa:Ga duk wanda yake da Zuciya (ta hankalta).To wannan shi ne Mahallin da zai karba, kuma abin nufi da shi shi ne Zuciya Rayayyiya wacce take fahimtar sakon AllahKamar yadda Allah Madaukakin Sarki ya ce:Lallai cikin wann nan ba komai ba ne face wa'azi sa kuma Qur'ani mai bayani domin a wa'azantar da RayayyeAi mai rayayyiyar zuciyaSannan fadinsako wanda aka jefa masa jiAi wanda ya bada jinsa kuma yai saurara da jinsa zuwa abinda ake fada a gare shi, kuma wannan sharadin yana tasiri wajen maganaSannan fadinsakuma yana mai halarto da ZuciyarsaAi yana mai harto da a Zuciyarsa baya kautar da itaIbn Kutaibah ya ce:Ka saurari Littafin Allah kuma yana mai halarto da Zuciyarsa da fahimta baya rafkana ko mantuwakuma wan nan yana nuni zuwa abin da yake hana tasirantuwa, kuma shi ne rafkanar zuciya da buyanta ga barin fahimtar abinda ake fada mata da kuma Nazari a cikinsa da yin kyakkayawan Duba to idan aka samu maisa tasirin shi ne Al'qur'ani kuma aka samu wurin karba shi ne zuciya rayayyiya, kuma aka samu sharadin shi ne sauraurarawa, kuma aka kore Mai hanawa shi ne shagaltuwar zuciya da kuma sakwarkwacewar ta daga Ma'anar Kira, da kuma kaucewarsa daga kan turba zuwa wani abu daban, sai tasirin ya faru shi ne anfanuwa da kuma wa'azantuwa.

Ina rokon Allah da ya amfanar da wannan littafin kuma ya sanya shi mai albarka kuma ya datar da Marubucinsa ga dukkan Alkairi

Tsira da Aminci ga Annabinmu Muhammad

Wanda ya rubuta shi: Abdullahi Bn Abdurrahaman Al'sa'ad

17/3/1428 Bayan Hijira

# Gabatarwa Babban Malami Masanin Hadisi Dr. Mahir Bn Yaseen Al'fahl Allah ya tsare shi

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin kai

Dukkan Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai kuma tsira da Aminci su tabbat ga Shugabanmu Annabi Muhammad da Alayansa da Sahabbansa baki Daya

Bayan haka

To lallai wajibin kira zuwa ga Allah yana daga cikin Mafi Cancantar Wajibai, kuma mafi wajabcin Biyayya ga AllahKuma Allah Madaukakin Sarki ya ce: "Babu wata Magana mafi kyau kamar wanda yayi kira zuwa ga Allah kuma yayi aiki nagari kuma ya ce yana cikin Musulmi.Surat Fussilat 33To ya wajaba akan kowane Musulmi cewa ya tsaya da wannan Wajibin na Addini ga Al'ummarsaAllah Madaukakin

Sarki ya ce:Kace wannan shi ne tafarki na na kira zuwa ga Addinin Allah kan Basira ni da duk wanda ya biniSurat Yusuf:108kuma yana daga cinikin mafi girman Wajibai wajen isar da Addinin Allah Kwadaitarwa kan kare wahayi guda biyu Alqur'ani da Hadisi su ne Ginshikan Addini da kuma Mabubbugar Tafarki Madaidaici, kuma ruko da su shi yake samar da jin dadin Duniya da Lahira.Kuma Alqurani Maigirma shi ne mai rarrabewa tsakanin gaskiya da karya, da kuma tsakanin Haram da Halal da kuma tsakanin Rabauta da kuma Tabewa.Kuma Alqurani Maigirma yana Alkairai masu yawa da tarin Ilimai, domin koawane Alkairi da kuma Ilimi an samo shi ne daga cikin littafin Allah kuma shi ne Mai yalwar Ma'anoni da kuma girma.kuma shi ne wa'azin da Mutum zai wa'azantu da shi na Al'amuran Ubangiji da Akidar Musulunci ingantacciya, da kuma kyawawan halaye masu girma,kyawawa, da kuma kyawawan Ayyuka.kuma shi ne Wa'azi mai girma wanda ya ke mai shiga jiki, da kuma labari masu girma da kuma Zancen Ubangiji, kuma babu abinda yake gyara zuciya sai Zancen Ubangiji.

Sannan kuma cewa yana daga cikin abinda yake Jawo farin cikin Rayuwata in gabatar da wannan littafin mai daraja Hadisai Arba'in game da Alquran.ga Dan uwanmu Shiekh Ahmad Abdurrazak Al-Ibrahim Al-angary Allah ya datar da shi da dukkan Alkairi,

Kuma littafi ne duk da kanakantar girmansa da kuma takaitattun Kalmominsa littafi ne mai Girma kuma mai Amfani, kuma mai amfani ga kuma suna bukatar kwatankwacinsa wajen dawowa zuwa ga littafin Allah a wani irin zamani wanda fitintinu suka sauka ga Mutane wanda Allah ne kadai ya sansu

kuma an Buga wannan littafi sama da Bugawa kuma an fassara shi kuma wanda ya wallafa shi ya kyautata wajen tara shi da kuma Rairarye Hadisan sa

Kuma ina rokon Allah ya rubuta masa dacewa da kuma gamdakatar, don ya gabatarwa makaranta babbar Hidima da sake buga wannan littafi, kuma Dan uwa Marubucin yana da matukar sha'awa wajen hidimtawa Hadisan Annabi wajen koya da koyarwa da kuma Rairayewa.

Kuma a Karshe ina gabatar da godiyata Mai yawa ga Mai bincike akan ya zabo wannan littafi, da kuma gabatar da shi don hidimta masa da kuma kulawa da shi, kuma ina rokon Allah gareni da shi haka baki dayan Musulmi da kyakkyawan dacewa a cikin Hidimar wannan Addini ta hanyar yada Ilimin Shari'ah

Wanda ya rubuta shi

Dr. Mahir Yaseen Al'fahl

Malamin Hadisi da kuma Fiqhun Mazhabobi

a Kwalejin Iliman Musulunci - Jami'ar Anbar

10\6\1432 Daga Hijirar Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata ga Allah

# Wanda ya Rubuta: Dr. Hamad Al-Tamimi: Hadisai Arba'in game da Al'qura'ni

Wannan littafi ya futo ne "Hadisai Arba'in game da Al'qurani"kuma an bugashi da daukar nauyin Shiekh Abdullateef Bn Sulaiman Bn Abdullateef Al-Ibrahim Al-angari, kuma littafi ne babu irinsa a lokacinsa, kuma wanda ya wuce wadanda suka gabace shi

Wannan littafin yayi fuce a sunansa haka abinda ya kunsa, kuma Manyan Malaman Hadisi sunyi masa Shaida da cewa bashi da tsara kafinsa, bugu da kari ga ingancin Hadisan sa wadan da aka kawo a cikin sa da abin da ya kunsa, kuma Hakika Mawallafin wannan littafin yabi tsarin Bukari, kuma hakika ya sanya Babunan Unwaninsa ya tsamo su ne daga Hadisan da suka zo a cikinsa kuma an gabatar da shi ga gungun Malamai kuma wadanda suka gabatar da littafin Manyan Malaman Hadisi guda biyu Abdullahi Bn Abdurrahman Al-Sa'ad da kuma Saleh Bn Sa'ad Al-luhaidan,da Wasun su kuma sun yabe shi da kyakkayawan yabo, kuma mafi kyawunsa.

kuma hakika duk wanda ya sami kwafin wannan littafin to yayi bayaninsa sabida abinda yake cikinsa na fa'idoji masu yawa ga Daliban Ilimi cikin abin da yake da Dangantaka da littafin Allah Madaukakin sarki

Kuma Allah ya datar da Mawallafin littafin, kuma wanda ya buga liittafin, da wanda ya raba shi, da wanda yayi masa sharhi ya yadashi a tsakanin Daliban Ilimi ga dukkan abin da ya yake so kuma ya yarda da shi, lallai cewa shi ne Majibinta hakan kuma mai iko akan hakan.

Kuma wanda ya rubuta wannan shi ne Masoyin daliban Ilimi kuma mai jin tausayinsu

Wanda ya rubuta: Dr. Hamad Al-tamimi Hadisai Arba'in game da Al'qurani

- 9/5/2010 A ranar :- 25/5/1431

Madogara: Shafin yanar Gizo Al'alouka

# Gabatarwar Mawallafi

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin kai

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai, Kuma tsira da Aminci su tabbata ga Shugabanmu Annabi Muhammad da Alayansa da Sahabbansa baki daya.

Bayan haka

Wannan shi ne Nassin: Hadisai Arba'in game da Al'qurani, wanda ya kunshi Hadisai Arba'in wadanda suka inganta daga Annabi kan Falalar Alqur'ani da Hukunce Hukuncensa da kuma Ladabansa

Kuma nayi kokarin cewa zan sanya Hadisi mai makusanciyar Ma'ana kuma wanda yake Maisaukin bayani don yai saukin haddace shi kuma a amfana da shi da kuma aiki da shi

Kuma duk wanda lura da Hadisai wadan da suka zo cikin magana kan Alqur'ani da Falalolinsa, kuma cewa zai samu ba wai kawai sun kebanta bane da haddar Alqur'ani kawai.

Da kulawa da Harafansa da Tajwidinsa da kuma rerashi, cewa ma duk wanda yake karanta Hadisai kuma ya lura da su zai samu cewa sun zo ne da kwadaitarwarwa kan Ilimi da kuma aiki da shi, da kuma Hadda.

Kuma a karshe ina kiran Yan uwana Maza da Mata zuwa ruko da Alqur'ani da kuma Ingantacciyar Sunnah da kuma aiki da su a fili da boye da kuma barin duk abinda ya Saba musu na Bidi'a ko Sabo ko takaitawa.

Kamar yadda na nuna a wanna littafin Hakika an rarraba shi zuwa Fasalai Kamar haka:

Fasali na farko

Hadisan da suka zo kan falalar karatun Alqur'ani da koyar da shi

Fasali na Biyu

Hadisan da suka zo kan Ladabai da hukunce Hukunce

Fasali na Uku

Hadisan da suka zo kan falalar Haddace littafin Allah da ladan Ma'abotansa

Fasali na Hudu

Hadisan da suka zo kan kwadaitarwa kan kokarin kiyaye haddar Alqur'ani da kuma Tilawarsa

Fasali na Biyar

Hadisan suka zo ciki falalar son kyautata Murya wajen karanta Qura'ni

Fasali na Shida

Hadisan da suka zo don tsarkake niyya wajen yin aiki sabida Allah maigirma da Daukaka

Fasali na na Bakwai

Hadisan da suka zo a falalar wasu surori

Wannan kuma ina rokon Allah dacewa da kuma gamdakatar da Ikhlasi cikin fada da kuma aiki

Kuma ina rokon Allah Mai tsarki don ya gafarta mana da Iyayenmu da Dangina Rayayyu da Matattu daga cikin su da Malamanmu da dukkan Musulmi Maza da kuma Mata

Allah Salati ga Annabinmu Muhammad da Alayansa da sahabbansa baki daya

Wanda ya rubutashi

Ahmad Bn Abdurrazaq Bn Muhammad Bn Zaid Al Ibrahim Al-anqary

An rubuta shi a birnin Riyadh a ranar: 25 /12/1427 bayan Hijira

Lambar Waya: 500850965/00966

E-mail:a.al-ibrahim@hotmail.com

# Yadda ake Haddace Hadisai

## Na farko:

Manufa na haddar Hadisi shi ne Ilimi da kuma aiki da kauda Jahilci ga barin kai

## Na biyu:

Lallai cewa Hadisai sun sha banban ta wajen tsawo ko gajarta, Hakika Dan uwana mai girma cewa kai kana son tabbatacciyar Hadda a kwakwalwarka ba haddar da zata gudu bayan kwana biyu sannan ka manta ta

kuma ga wata hanya mai sauki ya kai Dan uwana

Ka dauki Hadisi daya sannan ka karanta shi sau uku, sannan ka gyara kusakuren larabcinka in akwai, sannan sai maimaita shi sau goma da sauri kadan

Ka kuma maimaita Hadisin daga karantawa 10-20 kana kallo kana mai hararo Nassin, sannan ka maimaita shi 10-30 sai dai wannan a zuci

kayi kokari ka maimaita abinda ka haddace a kowane hali a tsaye ne ko a zaune da kafin bacci da kana hanyarka zuwa Masallaci tabbas zaka samu romon hakan in Allah ya so

kayi kokari ka kiyaye waje maimaita abinda ka haddace sau dari kuma ko yaushe adadin karantawa ya karu to haddar zata dada tabbata

kuma daga cikin ya wajaba bayaninsa cewa Mutane sun sha banban wajen hadda kuma kowanne hali ka sami kanka zaka samu lada kan hakan in Allah ya so

# Gabatarwar Littafin

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin kai

Dada Sarkin Muminai Baban Hafsu Umar Dan Khattab Allah ya yarda da shi ya ce:Naji Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ceDukkan ayyuka sai da niyya kuma kowane Mutum da irin niyyar da yayi to duk wanda yayi Hijira sabida Allah da Manzonsa to ladan sa yana ga Allah da Manzonsa, kuma duk wanda yayi Hijira domin neman Duniya ko wata mata da yake son Aura to ladan Hijirarsa yana ga abinda yayi Hijira sabida shi.Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi

Ta'aliki:

Mawallafin ya ce: cewa na fara da wannan Hadisi ne sabida koyi da magabatanmu, da kuma koyi da Limamin masu Hadisi babu mai ja kan hakan shi ne Abu Abdullahi Albkhari a cikin Sahihinsakuma

hakika magabata sun kasance na wannan Al'umma suna son bude littafi da wannan Hadisin kamar yadda Imam Abdurrahman Bn Mahdi - Allah ya yarda da shi - Duk wanda yaso wallafa wani littafi to ya fara da Hadisin Umar bn Khattab - Allah yarda da shi - Cewa kowane aiki sai da Niyya a cikin kowane BabiTo sabida haka na fara littafi na Hadisai Arba'in da suke Magana kan Alqurani, don fadakar da kaina da kuma mai karatu da kuma Dalibi kan gyara Niyya, cikin Ayyukanmu Na fili da na boye

# Fasali na farko

## Hadisan da suka zo kan falalar karatun Alqur'ani da koyar da shi

### Hadisin farko

Falalar Koyar da Alqur'ani

Daga Abu Huraira Allah ya yarda da shi ya ce:Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya cekuma wasu Mutane basu hadu a wani daki daga cikin Dakunan Allah ba suna karanta littafin Allah kuma suna koyar da shi a tsakaninsu sai nutsuwa ta sauka a kansu kuma Rahama ta rufe su kuma Mala'iku sun kewaye su kuma Allah ya ambace su cikin wadanda suke gurinsa, kuma duk wanda aikinsa ya maida shi baya to dangantakarsa ba zata shi yayi gaba baMuslim ne ya Rawaito shi da Kuma Abu Daud da kuma wanin su

Ta'aliki:

Wannan Hadisi ya bai kunshi Jama'ar ba kawai ya game daidaiku ma da ace Mutum daya zai zauna shi kadai kuma ya ambaci Allah to zai sami wannan Falalar da aka ambata.

## Hadisi na Biyu

Kowane Harafi daya daga littafin Allah za'a bada ladan kyawawan ayyuka goma

Daga Ibn Mas'ud Allah ya yarda da shi ya ce:Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ceDuk wanda ya karanta littafin Allah to yana da lada kuma kowane lada za'a ninkashi goma amma bazance Alif lameem harafi daya bane, sai ince Ali harafi Meem harafi neTurmizi da Al-darimi ne suka Rawaito kuma Abu Isa ya ce wannan Mai kyau ne kuma ingantacce kuma GharibiKuma Albani ya inganta shi, kuma na tambayi Malaminmu Abdullahi Al'sa'ad game da shi ya: bashi da wani aibi.

## Hadisi na Uku:

ceton Alqurani ga Ma'abotansa Ranar alkiyama

Daga Abu Umama Allah ya yarda da shi ya ce:Naji Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ceKu karanta Alqurani domin zai zo Ranar Alkiyama mai ceton Ma'abotansaMuslim ya raaito shi

Ta'aliki:

A cikin wannan Hadisi tabbatar da ceton Alqurani a ranar Akiyama bisa sabanin ceton da masu ceton .Kuma ceto ba zai yiwu sai ga Masu Kadaita Allah amma Mai shirka bashi da wani ceto koda kuwa ya fi kowa Haddar Qur'ani Domin aikinsa an bata shi tun daga Duniya sabida Shirka kuma ba za'a taba karbar komai daga gare shi ba a lahira, Allah ya tsare mu daga Shirka da masu yinta

## Hadisi na Hudu:

Kwatankwacin Muminin da yake karanta Alqurani da Munafikai

Daga Abu Musa Al'ash'ary Allah ya yarda da shi ya ce:Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ceKwatankwacin Muminin da ya ke karanta Alqur'ani kamar lemon Zaki ne Kanshin dadi haka ma Dandanonsa, kuma kwatankwacin Muminin da baya karanta Alqur'ani kamar Dabino ne bashi da kanshi amma dandanonsa Zaki, kuma Munafikin da yake karanta Alqurani kamar Nana ne kanshinsa

dadi amma dandanonta daci, kuma kwatankawacin Munafikin da baya karanta Alqura'ni kwatankwacin Guna ce batada Kanshi kuma dandanonta daci.Muslim ya Rawaito da Buhari kuma sun hadu a lafazin Fajiri a maimakon - Munafuki

Ta'aliki:

Kwatankwacin Lemon Tanjirin

Kwatankwacin Lemon Tanjirin ya hade dadin dandano da kuma dadin Kamshi kuma ana kiransa da lemon zaki

Guna

Guna: wani tsiro ne da yae yado akan Kasa kamar kankana, kuma "ya'yan sa sunyi kama da na Kankana sai dai su kanana ne tayi fuce wajen Daci

## Hadisi na Biyar

Ladan Gangaran a Qur'ani da kuma wanda yake guragura a cikinsa

Kuma daga Nana Aisha Allah ya yarda da ita ta ce:Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ceGangaran wajen Karatun Quran yana tare da Manyan Mala'iku Masu biyayya ga Allah, kuma wanda yake karatu kuma yake guragura a cikinsa yana mai shan wuya to yana da lada biyu.A kuma cikin wata RiwayarWanda yake karanta shi kuma yana yi masa wahala akansa yana da lada biyuBuhari da Muslim ne suka rawaito amma lafazin na Muslim ne da kuma Ma'abotan Litattafan Sunan

Ta'aliki:

Gwanin Alqurani

Shi ne Haziqi kuma mai iya Tajawidi wanda yake karatu ba tare da tantama ba ko kusakurai kuma bayajin wahalar karatun sabida kyawun Haddarsa da Karatun sa

Kuma yake guragura a cikin karatun sa

Shi ne wanda yake gura gura a cikin karatunsa don raunin Haddarsa to yana da lada biyu ladan Karatu da ladan wahalar karatun da wahalarsa

## Hadisi na Shida

Falalar Karatun Alqurani a cikin Sallah

Daga Abu Huraira Allah ya yarda da shi ya ce:Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ceShin dayanku yana son idan ya koma ga Iyalansa ya Taguwoyi Uku Masu ciki Manya ? sai muka ce ey sai ya ce to Ayoyi Uku da zai karanta su a cikin Sallarsa to sunfi Taguwoyin Uku Masu ciki kuma Manya.Muslim ya raaito shi

Ta'aliki:

Takuwa Mai Ciki kuma Babba kuma anai mata Jam'i da Taguwoyi

## Hadisi na Bakwai

Falalar Wadan da suke aiki da Qur'ani

Daga Nawwas Dan Sam'an Allah ya yarda da shi yana cewa:Naji Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ceZa'a zo da Qur'ani a ranar Alkiyama da kuma wadan da suke aiki da shi Suratul Baqara tana yi musu jagora da Suratu Aal Imran, kuma Annabiya buga Misali guda uku da su, kuma ban manta da su ba, ya ce: Kamar Gizagizai, suna masu masu Duhu, a tsakaninsu da wani Haskekai ka ce Tawagar tsuntaye ne sun yi Sahu, suna kare Ma'abocinsu.Wannan lafazin Ahmad ne da Muslim daga Ishak Bn Mansour ya ce: Yazid Dan Abdu Rabbih ya bamu Labari da wannan Sanadin sai dai ya canza dai dai Tana yi musu Jangora, a Maimakon tana Jayayya.Daga Abu Musa Allah ya yarda dashi daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi ya ce:Kwatankwacin

Muminin da yake karanta Alqur'ani kuma yake aiki da shi Kamar Lemon Zaki Dandanonsa Zaki da haka Kanshinsa, kuma kwatankwacin wanda baya Karanta Al'qur'ani kuma yake aiki da shi Kamar Dabino ne Ga dadin Dandano kuma bashi kan shiBuhari ne ya rawaito shi

Ta'aliki:

Ibn Al-qayyim ya ce:Ma'abotan Qur'ani su ne Masanan sa kuma masu aiki da shi koda kuwa basu haddace shi ba a kwakwalwarsu, kuma duk wanda ya haddace shi bai kuma fahimce shi ba kuma baya aiki da shi ba to baya cikin Ahalinsa kuma duk wanda ya iya Harafansa iyawa,Zaad Al'Ma'adKuma Annabi tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi ya ce:Kai kace Gizagizai guda biyuAi ladan Surorin Bakara da Ali Imran Kamar wadansu giza gizai Manya guda biyuKo gigizai biyu Bakake a tsakaninsu akwai HaskeSabida Bakinsu da haduwar su da wasu da suke saman wasu don yin Inuwa ga Mai karanta shi a ranar alkiyama daga zafin RanaSannan fadinsaA tsakaninsu akwai hasken RanaAi Hasken Rana da Annuri shi ne Hasken Rana don fadakarwa kan cewa su duk da kaurinsu amma basa boye Haske.ko Kamar Garke biyu ko Wata TawagaAi Garke biyu ko Wata TawagaDaga Tsuntsaye da suke SahuAi sun yi Sahu Kamar yadda Masu Sallah suke yiSuna Jayayya da kuma kariyaAi Suna Jayayya da kuma kariyaGa Ma'abocinsuWanda ya kasance ya dawwama wajen Karatun Alqur'ani kuma yana aiki da shi

## Hadisi na Takwas

Falalar Karatun Surat Albakara a cikin gida

Daga Abi huraira Allah ya yarda dashi daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi ya ce:Kada ku Mayar da gidajenku Makabarta Cewa Shaidan yana guduwa daga gidan da ake karanta Surat Al-baqaraMuslim ya rawaito shi

## Hadisi na Tara

Falalar Mai Bayyanawa da Mai Asirta Alqur'ani

Daga Uquba Dan Amir Aljuhani Allah ya yarda da shi ya ce:Naji Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa:Wanda yake bayyana karatun Alqur'ani Kamar mai bayyana Sadakarsa ne kuma mai boyewa kamar Mai boye Sadakarsa neTirmithi ne ya Rawaito shi da Abu Daud da Ahmad da kuma Nasa'iAbu Isa Attirmidhi ya ce: Wannan Hadisi ne Hasan Garib kuma Albani ya Inganta shi

## Hadisi na Goma

Son Saurarón Qurani

Daga Ibn Mas'ud Allah ya yarda da shi ya ce:Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce da niKarantamun Alqur'ani Sai ya ce: Ya Manzon Allah in karanta Maka bayan kai aka saukarwa sai ya ce ni ina sha'awar inji shi daga bakin wani na sai na karanta Surat Al'nisa har nakai dai daiTo yaya idan Muka zo daga koawace Al'umma Mai mata Shaida kuma muka zo dakai mai shaida ga Wadan nan.Sai na daga kaina ko ya zungureni a gefena sai na daga kaina sai naga hawayansa suna kwaranyaMuslim da Buhari ne suka rawaito shi amma lafazin na Muslim ne

# Fasali na Biyu

## Cikin Ladabai da kuma Hukunce Hukunce

### Hadisi na sha Daya

Burin Zamatowa Wani daga cikin Ma'abotan Alqur'ani

Daga Abi huraira Allah ya yarda dashi daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi ya ce:Babu Hassada sa a abubuwa biyu: Wani Mutum da Allah yasanar da shi Alqur'ani yana karantashi cikin dare da kuma Rana sai wani Makwabcinsa yaji shi sai yace ina ma dai nima anbani irin abinda aka bawa wane inyi irin yadda yake yi da wani Mutum da Allah ya bashi Dukiya kuma yana

karar da ita a hanyar Gaskiya sai ya ce: ina ma ace ina da kwatankwacin dukiyar wane inyi irin yadda yake yiBuhari da Ahmad suka rawaito shi amma lafazin na Buhari ne

## Hadisi na Sha Biyu

Yadda Annabi yake Karanta Alqur'ani

Daga Huzaifa Allah ya yarda da shi cewa Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi yayi sallahya kasance idan ya wuce Ayar Azaba yana tsayawa ya nemi tsari kuma idan ya wuce Ayar Rahama sai ya tsaya kuma yayi Addu' kuma idan ya wucce tsarkake Allah sai yai TasbihiIbnu Maja ya rawaito shi kuma Albani ya inganta shiKuma daga shi dai cewa Allah ya yarda da shi nayi Sallah a gefen Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi wani dare sai ya karanta, ya kasance idan ya wuce Ayar Azaba yana tsayawa ya nemi tsari kuma idan ya wuce Ayar Rahama sai ya tsaya kuma yayi Addu'a.Nasa'i ya rawaito shi kuma Albani ya inganta shi

## Hadisi na sha uku

Tsawon lokacin da yake sauke Alqur'ani

Daga Abdullah Dan Umar Allah ya yarda da shi cewa Annabi ya ce da shi ka karanta Qur'ani a wata daya, sai ya ce nidai bani da karfi, sai ya ce ka karanta cikin kwana ashirin, sai ya ce bani kwarin hakan sai ya ce: to cikin kwana goma sha biyar sai yace bana jin kwarin hakan, to ka karanta cikin kwana goma, sai ya ce n bani da kwarin hakan sai ya ce ka karanta cikin kwana bakwai, kuma kada ka kara kan hakan.Buhari da Muslim suka rawaito shi da kuma Abu Daud kuma lafazin na Abu Daud ne

Ta'aliki:

wannan Hadisin daga abubuwan da Abdullahi Dan Amr Asi cewa Annabi ya shiryar da shi yayin da yaga halinsa da kuma ikonsa don haka lokacin da Abdullahi Dan Umar ya tsufa sai ya koma yana shan wahalar abinda ya saba da shi sabida yawan karatunsa da kuma aikiSai ya ce Allah ya yarda da shi Kamar inda yake a cikin BuhariIna ma dai ni na karbi saukin Annabi kuma wancananka gani na tsufa kuma nayi rauni sai ya kasance yana sauke Alqur'ani tare da Ahalinsa a kwana bakwai kuma wanda zai karanta shi da daddare sai ya karanta shi da Rana don ya samu saukin sa da daddare kuma idan yana son ya samu karfin jikinsa sai ya sha ruwa kwanaki, yana kidanyasu kuma sai ya Azumci kwatankwacinsu don tsoron kada yabar komai bayan sun rabu da Annabi yana yinsa.

Na bayyana wannan Al-amari a nan kada wani ya zaci cewa wanda ya sauke Qur'ani daga cikin Sahabbai a kwana daya ko kwana biyu wannan ya sabawa abin da Annabi yayi Umarni da shi Abdullahi Bn Amr, Ba haka abin ya ke ba kuma Jawabin hakan shi ne cewa Annabi ya Amsawa mai tambaya dai dai da halinsa da mai neman neman fatawa na Musamman Kuma tsamo Hukunce Hukunce da kuma Dalilai na baki daya, sai Hadisin cikinsa akwai Kebancewa da gamewa.

## Hadisi na Sha Hudu

Anso idan Mutum ya wuce Ayar Sujada yayi Sujadar

Daga Abu Huraira Allah ya yarda da shi ya ce:Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ceIdan Dan Adam ya karantaMuslim ne ya rawaito shiA cikin Al'sunna na AlbagawiSai ya ce kaito na an Umarci wannan da yayi Sujada ...

Ta'aliki:

Sujada ba wai tana hade da Surar sujada bane kawai, aa tana hade da baki dayan Sajadodin wadanda suke cikin Qurani wadanda suke sujada goma sha biyar

## Hadisi na sha biyar

Sabida kin daga da Qurani idan za'a cutar da wadanda suke gefe

Daga Al'bayadi Allah ya yarda da shi cewa Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya futo ga Mutane suna Sallah suna daga Muryarsu da Karatu sai ya ce:Lallai mai Sallah yana ganawa da

ubangijinsa to yasan da wa yake ganawa kuma kada dayanku ya daga Murya kan daya wajen karanta Qur'aniAhmad da Malik da Nasa'i daBaihaki suka rawaito shi kuma Alhaithami ya Inganta shi

## Hadisi na sha shida

Halayen Annabi tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi

Daga KatadaYa Uwar Muminai ki bamu labarin Halayen Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shiTa ce: Ba kana karanta Qur'ani ba ? sai nace ina karantawa sai ta ce: to Halayen Annabin Allah sun kasance irin Halayen Qur'ani neMuslim ya raaito shiDaga Sa;ad Bn Hisham Bn Amir ya ce:Naje wajen Aisha Allah ya yarda da ita sai na ce:Ya Uwar Muninai ki bamu labarin Halayen Annabi tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shiTa ce:Halayansa sun kasance Alqurani ne, baka karanta fadin Allah Mai girma da daukaka ba ne?Kuma, lalle haƙiƙa kana a kan hãlãyen kirki, manya.Surat Alqalam Aya ta 4Ahmad ya rawaito shi kuma Hadisi ne ingantacce

Ta'aliki:

Ibn Kathir ya ce:Abin da ake nufi da wannan cewa Annabi Amincin Allah a gare shi ya zamanto yana aiki da umarni da hanin qur'ani hakan ma ya zamar masa Dabi'a da halitta har takai ya bar Dabi'unsa na Asali ko yaushe aka hana shi wani abu sai ya hanu ga kuma kyawawan Dabiu da Allah ya gina shi akansu Masu girma na kunya da Karamci da kuma sadaukantaka da Kauda kai da dukkan kyawawan Halaye kamar yadda ya Tabbata.Tafsirin Surat Alqalam

## Hadisi na Sha Bakwai

Halarcin karanta Alqurani akan Dabba da kuma halarcin Maimaita Aya a cikin sa

Daga Abdullahi bn Mugaffal Al'muzni Allah ya yarda da shi ya ce:Naga Manzon Allah a Ranar Bude garin Makkah yana kan Taguwarsa yana karanta Surat Al'fath kuma yana Maimaita AyoyinBuhari da Muslim suka rawaito shi da kuma Abu Daud kuma lafazin na Abu Daud ne

Ta'aliki:

Tarji'a

o, yãyã, idan Mun zo da shaidu daga dukkan al'umma, kuma Muka zo da kai a kan waɗannan, kana mai shaida!o, yãyã, idan Mun zo da shaidu daga dukkan al'umma, kuma Muka zo da kai a kan waɗannan, kana mai shaida!Maimaita Karatu: irinsa ne dai Maimaita kiran Sallah

## Hadisi na ShaTakwas

Hanin tafiya da Qur'ani zuwa garin Kafirai da Abokan gaba idan aka ji tsoron tozarta shi a Hannunsu

Daga Abdullahi Dan Umar ya ce:Annabi ya hana tafiya da Qur'ani zuwa garin Abokan GabaBuhari Da Muslim suka rawaito shiA wata riwayar kuma ta Muslim daga Nafi'u daga Dan Umar ya ce:Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ceKada kayi tafiya da Qurani don ni bana amince maka Abokan gaba ba zasu tozarta shi ba

Ta'aliki:

Malamai sun ce:

Idan aka aminta cewa Qurani ba za'a yaga shi ba ko a jefar da shi a kasa ko Kafiri ya taba shi to halarta ayi tafiya da shi

## Hadisi na sha tara

yaya zai yi wanda ya rkirkice a karanta Qur'ani sabida tsananin Gyangyadi

Da hadisin Abi huraira Allah ya yarda dashi daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi ya ce:Idan Dayanku o, yãyã, idan Mun zo da shaidu daga dukkan al'umma, kuma Muka zo da kai a kan waɗannan, kana mai shaida!Muslim da Ahmad da Abu Daud da Ibn Majah da Nasa'i ne suka Rawaito da wasun su ma

Ta'aliki:

FadinsaSai yake ta bata Al'quraniAi ya kasa ci gaba kuma harshensa ya rike sabida yawan Gyangyadi sabida haka sai ya bar karatun

## Hadisi Na ashirin

Fadin Mai koyar da karatu ga Mai Mai karatu Ya isa haka

Daga Ibn Mas'ud Allah ya yarda da shi ya ce:Manzon Allah tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce da ni:Karanta mun sai na ce: o, yãyã, idan Mun zo da shaidu daga dukkan al'umma, kuma Muka zo da kai a kan waɗannan, kana mai shaida!To, yãyã, idan Mun zo da shaidu daga dukkan al'umma, kuma Muka zo da kai a kan waɗannan, kana mai shaida!Ya ce Ya Isheka yanzu sai ya waiwaya zuwa gare shi sai ya ga idanunsa suna zubar da hawayeBuhari ne ya rawaito sho

# Fasali na Uku

## Hadisan da suka zo kan falalar Haddace littafin Allah da ladan Ma'abotansa

### Hadisi na Ashirin da Daya

Cewa duk wanda ya koyi Al'qurani kuma ya koyar da shi ya kasance mafificin a cikin wannan Al'umma kuma mafi Alkairin ta

